Food and Agriculture Organization of the United Nations

Global Soil Doctors Programme

## Sinadaran kasa – Gwaji na C01a

# GANE DANDANON KASA TA HANYAR ANFANI DA COLORIMETRIC INDICATOR DA DUNIYA TA YARDA DASHI

## Fastar la'akari na 12a-12b-12c

| | | |
|---|---|---|
| MUHIMMANCI | Dandanon kasa Shine ma'aunin sinadaran da kasa take dashi dake taka muhimmiyar rawa wajan daidaita samuwar sinadaran da kuma sauran al'amuarn dake faruwa a kasar. Ana samun sinadari guda daya da shuka ke tsotsa a ma'aunin dandanon kasa mabanbanta saboda haka amfanin gona daban-daban suna bunkasa akan ma'aunin dandano daban-daban. Ya kama daga ma'aunin dandano 5.5 da 7.5 sun dace da yawancin amfanin gona saboda suna iya tallafawa nau'ikan abubuwan gina jikin shuka da yawa. Idan Kimar dandanon kasa bai kai 7 ba, na nuna kasa tana da gishiri sama da bakwai kuma kasa tanada kanwa. Anan, abin gwada dandanon kasa Wanda aka kirkiro kuma aka samar dashi daga bangaren kimiyyah domin bunkasa kasa na kasar Thailand shi akayi amfani domin tnatance dandanon kasa | |
| KAYAN AIKI |  Kayan gwajin dandanon kasa  | |
| TSARI (HANYOYI) | 1) Dibo nau'in kasa na wuri daya ko fiye. Sanya nau'in kasar a farantin gwaji, a tabbatar da cika abinda bai wuce rabin kowani alama ba da kasan. |  |
| | 2) Zuba yan digon ruwan dake nuna hadi akan nau'oin kasar har sai ta jike. |  |
| | 3) Yi amfani da Spatula (abin diban kasa) Ka cakuda kasar da ruwan dake nuna hadi sosai. Ana iya kara ruwan dake nuna hadin idan akwai bukata. |  |



GLOBAL SOIL PARTNERSHIP

| | | |
|---|---|---|
| | 4) A barbada hodar akan nau'oin kasar sai kuma a jira nayan mintoci kadan don launin ya bayyana. |  |
| | 5) Kwatanta launin da akasamu tare da Jidauwalin karanta dandanon kasa da aka bayar. Ka zabi mafi kusancin launin a ciki minti uku sannan ka karanta adadin kimar dandanon kasar da aka samu. |  |
| AMFANIN WANNAN HANYAR | Saukin tantancewa, babu bukatuwar wani ilimi na musamman. Samun sakamako dai-dai. Iyakwatanta (gwada) nau'ikan kasa daban-daban a chikin kankanin lokaci. | |
| GAZAWAR WANNAN HANYAR | Iyakantaccen adadin karatune kawai zai yiwu saboda baza a iya sake zuba kwabin ba (ri-egent). Daidaita launukan sai sun zama zahiri. Bai dace ba idan ana bukatar ainihin kimar dandanon kasa. | |
| TAMDAYOYI DA ZA A AMSA | Menene dandanon kasar da aka gwada?<br>Yayi kadan ko yayi yawane? Menene sakamakon hakan akan shuka?<br>Shin akwai hanyar inganta dandanon kasar.<br>Baya ga wadatuwar sinadaran habaka shuka, wadanne abubuwane kuma dandanon kasa zai iya shafan wanzuwan su ? | |

| MISALAN KWATANTAWA (GWAJI)<br>(Ya danganta abinda shuka ke bukata) | | |
|---|---|---|
| MARA KYAU | MATSAKAICI | MAI KYAU |
| Kimar dandanon kasa da 4 ko sama da 8. Gishiri ko kanwa yayi yawa. | Kimar dandanon kasa kasa da 5.5 ko sama da 7. Yayi gishiri ko kanwa kadan | Kimar dandanon kasa daga 5.5 zuwa 7. Kasa tsakatsaki kenan. |

[1] Soil testing method manual https://www.fao.org/documents/card/en/c/ca2796en